Mutane ba zasu gushe ba cikin alheri matuƙar sun gaggauta buɗa baki

Daga Sahl ɗan Sa'ad - Allah Ya yarda da shi - lallai Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Mutane ba zasu gushe ba cikin alheri matuƙar sun gaggauta buɗa baki".
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bada labarin cewa mutane ba za su gushe ba a cikin alheri muddin dai sun gaggauta buɗa baki a azimi, bayan tabbatar da faɗuwar rana; hakan dan ruko da sunna, da tsayuwa a iyakarta.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/4438